# 6

# Siffar Yadda Ake Sallah

## Fuskantar Alƙibla Da Kabbarar Harama

- Wanda zai yi sallah zai tsaya, yana mai fuskantar alƙibla, yana mai jin tsayuwarsa gaban Allah Maɗaukakin Sarki, mai ƙasƙantar da kansa a cikin sallarsa.

- Sannan sai ya yi niyyar sallah a cikin zuciyarsa.

- Sai ya ɗaga hannayensa daidai kafaɗunsa ko kunnuwansa, ya ce «Allahu Akbar» (Muslim ne ya rawaito shi).

- Sannan sai ya sanya hannunsa na dama akan na hagu a kan ƙirjinsa, ko kuma ya riƙe hannun hagu da damansa.

## Buɗe Sallah Da Karatun Fatiha

- Mai sallah zai sunkuyar da kansa, ya sanya ganinsa zuwa inda zai yi sujjada, sannan ya ce, «Subhanakal Lahumma Wabi Hamdika, Tabarakas Muka, Wata'ala Jadduka, Wala'ilaha Gairaka» (Muslim ne ya rawaito shi).

- Sannan bayan haka sai ya ce,«A'uzu Billahi Minash Shaiɗanir Rajim, Bismillahir Rahmanir Rahim»(Muslim ne ya rawaito shi).

- Bayan haka sai ya karanta fatiha, ya ce, «Amen» (A Karshen ta) Ma'ana Allah ka amsa.

- Sannan sai mai sallah ya karanta fatiha da sura, ko kuma abin da ya sauwaƙa daga Alƙur'ani a raka'a biyun farko, ya bayyana karatu a sallar asuba, da raka'o'in biyun farko a sallar magariba da isha.

### Abubuwan Da Ke ciki


Fuskantar Alƙibla

Buɗe Sallah Da Karatun Fatiha

Ruku'u Da Ɗagowa Daga Ruku'u.

Sujjada Da Ɗagowa Daga Sujjada

Tahiya

Sallama

Zikiri Bayan Sallah




https://www.al-feqh.com/ha

# Ɗagowa Daga Ruku'u

- Mai sallah zai ɗaga hannayensa, yana mai kabbara, ya tafi ruku'u, ya sanya hannayensa akan gwiwowinsa, yana mai buɗe 'yan yatsunsa, yana mai damƙar gwiwowinsa, ya daidaita bayansa da kansa, sannan ya ce, «Subhana Rabbiyal Azim» (Tirmizi ne ya rawaito shi) sau uku.

- Sannan sai ya ɗago ya ce, (Liman ne ko wanda yake yi shi kaɗai) «Sami'allahu Liman Hamidahu» (Tirmizi ne ya rawaito shi ya ce, (kowa da kowa) : «Rabbana Walakal Hamdu, Mil'as Samawati, Wa Mil al'ard, Wa Mil'a Ma Baina huma, Wa Mil'a Ma Shi'ata Min Shai'in Ba'adu»(Tirmizi ne ya rawaito shi). An so ya ɗora hannayensa akan ƙirjinsa, kamar yadda ya yi kafin ya yi ruku'u.



# Sujjada Da Ɗagowa Daga Gareta

- Mai sallah zai yi kabbara, sannan ya tafi zuwa sujjada, ya zama farkon abin da zai fara sauka a kan ƙasa gwiwowinsa, sannan hannayensa, sai goshinsa da hancinsa, ya shimfiɗa tafukansa akan ƙasa, (ya sanya su) daidai da kunnuwansa ko kafaɗunsa.

Ya sanya 'yan 'yatsun hannayensa su kalli alƙibla, ya ɗaga tsintsiyar Tsintsiyar Hannu ita ce abin da yake tsakanin tafi zuwa gwiwa. hannunsa daga ƙasa, ya nisantar da dantsensa Dantse shi ne : Daga Gwiwar Hannu zuwa kafaɗa daga geffensa, cikinsa kuma daga cinyoyinsa, ya ce, «Subhana Rabbiyal A'ala»(Muslim ne ya rawaito shi) sau uku, ya yawaita addu'a a cikin sujjadarsa.

- Sannan ya ɗago kansa yana mai kabbara, kada ya ɗaga hannayensa, ya zauna yana mai shimfiɗa ƙafarsa ta hagu, ya kafe ta dama, ya sanya 'yan 'yatsun ƙafafun nasa su kalli alƙibla, ya ce,«Allahummag firli, War'amni, Wajburni, Wahdini, Warzuƙni» (Tirmizi ne ya rawaito shi).



https://www.al-feqh.com/ha

- Sannan ya yi kabbara, ya yi sujjada ta biyu kamar yadda ya yi ta farko.

- Sannan sai ya ɗago kansa yana mai kabbara, ya zauna ɗan kaɗan, zaman da ake kiransa da «Jilsatul Istiraha» Saboda hadisin Malik ɗan Huwairis – Allah ya yarda da shi – a wajen siffata sallar Manzon Allah (S.A.W) cewa shi Manzon Allah (S.A.W) «Bai miƙe ba (daga sujjada) har sai da ya daidaita a zaune» (Bukhari ne ya rawaito shi).

- Sannan sai ya tashi zuwa raka'a ta biyu yana mai kabbara, mai dogaro akan hannayensa.

- Ya sallaci raka'a ta biyu kamar yadda ya yi ta farko, sai dai ba zai faɗi addu'ar buɗe sallah ba.

## Tahiya

- Idan mai sallah ya gama raka'o'in biyun farko sai ya zauna don yin tahiyar farko, yana mai shimfiɗa ƙafarsa da hagu, ya kafe ta dama, ya sanya hannayensa akan cinyoyinsa, ya shimfiɗa hannunsa na hagu, ya kame ɗan ƙaramin 'yatsansa da mai bi masa da na tsakiya, ya ɗaga ɗan 'yatsansa manuniya, ya yi nuni da shi yayin tahiya, ya riƙa kallonsa ya ce,«Attahiyyatu Lillahi, Wassalawatu, Waɗɗayyibatu, Assalamu Alaika Ayyuhan Nabiyyu, Warahmatullahi Wabarakatuhu, Assalamu Alaina Wa'ala Ibadullahis Salihina, Asshahadu An la'ilaha Illah Lahu, Wa Asshahadu Anna Muhammadan Abduhu Warasuluhu» (Bukhari ne ya rawaito shi).

- Sannan ya miƙe yana mai kabbara, ya ɗaga hannayensa yayin kabbarar, ba zai karanta komai ba a sauran raka'o'in sai fatiha kaɗai.



https://www.al-feqh.com/ha

- Ya zauna a harɗe a tahiyar ƙarshe, Ma'ana ya zuro ƙafarsa ta hagu daga bangaren damansa yana mai shimfiɗata, ya zauna akan mazaunarsa, ƙafarsa ta dama kuma ya kafe ta, ya faɗi abin ya zo a tahiya ta farko, ya ƙara a kai da cewa : «Allahumma Salli Ala Muhammad, Wa'ala Aali Muhammad, kama Sallaita Ala Ibrahim, Wa ala Aali Ibrahim, Innaka Hamidun Majid. Allahumma Barik Ala Muhammad, Wa'ala Aaali Muhammad, Kama Barakta Ala Ibrahim, Wa'ala Aali Ibrahim, Innaka Hamidun Majid» (Bukhari ne ya rawaito shi).

- Sannan ya ce, «Allahumma Inni A'azu Bika Min Azabi Jahannama, Wamin Azabil Kabri, Wa min Fitnatil Mahya Wal Mamati, Wa min Sharri fitnatil Masihil Dajjal» (Bukhari ne ya rawaito shi).

## Sallama

A ƙarshe, mai sallah zai yi sallama a ɓangaren damansa ya ce, «Assalamu Alaikum» a hagun sa ma hakan.

## Daga Cikin Zikiran Da Ake Yi Bayan Sallah

- - «Astagfirullahi» sau uku, «Allahumma Antas Salam, Wa minkas Salam, Tabarakta Yaa Zal Jalal Wal Ikram»(Muslim ne ya rawaito shi).

- «Laa ilaha Ilal Lahu, Wahdahu La sharika Lahu, Lahul Mulku, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai'in Kadiir. Allahumma La mani'a lima aaɗaita, Wala mu'uɗiya lima Aaɗait, Wala Yanfa'u Zal Jaddi Minkal Jadd»(Bukhari ne ya rawaito shi).

- «Laa ilaha Ilal Lahu, Wahdahu La sharika Lahu, Lahul Mulku, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai'in Kadiir. La haula wala ƙuwwata illa billahi, Laa ilaha illal Lahu, Wala Na'abudu Illa Iyyahu, Lahun ni'imatu Walahul Fadlu, Walahus sana'ul Hasan, Laa ilaha Ilal Lahu, Mukhlisina lahudden, Walau karihal Kafiruun» (Muslim ne ya rawaito shi).

- «Subhanallah, Wal Hamdu Lillahi, Wallahu Akbar»(Muslim ne ya rawaito shi) Sau talatin da uku. «Laa ilaha Ilal Lahu, Wahdahu La sharika Lahu, Lahul Mulku, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai'in Kadiir»(Abu Dawud ne ya rawaito shi).

- «Allahumma A'inni Ala Zikrika, Wa shukrika, Wa Husni Ibadatika»(Nasa'i ne ya rawaito shi).



https://www.al-feqh.com/ha

- Karanta ayatul Kursiyyi, da suratul Al-ikhlas, da Falaƙi da Nasi.
- Faɗin «Allahumma Inni As'aluka Ilman Nafi'an, Wa zirƙan Ɗayyiban, Wa amalan Mutaƙabbalan» (Ibnu Majah ne ya rawaito shi)Bayan an yi sallah daga sallar asuba.

An karɓo daga Aisha – Allah ya yarda da ita – ta ce, Manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana buɗe sallah da kabbara, karatu kuma da «Alhamdu Lillahi Rabbil Aalamin». Hakanan ya kasance idan ya yi ruku'u baya ɗaga kansa sama, kuma baya sunkuyar da shi ƙasa, sai dai yana sanya shi tsakanin haka. Idan ya ɗago kansa daga ruku'u baya sujjada har sai ya daidaita a tsaye, hakanan idan ya ɗago daga sujjada baya komawa sujjada har sai daidaita a zaune. Ya kasance yana faɗin tahiya a dukkan tsakanin raka'o'i biyu. Hakanan ya kasance yana shimfiɗa kafarsa ta hagu, ya kafe ta dama (a zaman tahiya). Ya kasance ya hana zaman shaiɗan (zama akan dugadugai), yana hana mutum ya shimfiɗa tsintsiyar hannunsa kamar yadda dabbobi suke yi. Yana ƙare sallah da sallama»(Muslim ne ya rawaito shi)

## Mas'aloli :

- Wasu mutanen suna jin zafi da raɗaɗi idan suka yi zaman da ake so a tahiya da tsakanin sujjadu guda biyu, to irin waɗannan babu laifi a kansu su zauna zaman da za su iya, saboda wahala da tsanani suna kawo rangwame a shari'ar musulunci.
- Mace daidai take da namiji a wajen yadda ake yin sallah, komai-da-komai.

https://www.al-feqh.com/ha



Kabbara



Ɗora Hannu Akan Kirji



Ruku’u



Sujjada



Zama Tsakanin Sujjadu Biyu



Zaman Tahiya



Sallama

https://www.al-feqh.com/ha